# FALALAR ALKUR’ANI

*Mahmudul Kalaam* (+234 902 0194 569)

1. Kalikina Allah Wahidin
Kaine Sarkin da Ka daukaka.

2. Kay kasa, Ka zubar da rowan sama
Ya taho ta tudu yabi rafuka.

3. Kai, cinya, Kai kayi, har kafa
Kayi hannu Kai kayi tafuka.

4. Ka halicci damo mai hankuri
Kai ka kagi halittan karnuka.

5. Ka haɗamu da Manzo Annabi
Mahamudu Muhammadu mai Maka.

6. Ku sani, mu sani, su sani duka
Matsayinshi kwarai ya ɗaukaka.

7. Kukana Rabbi sanar da ni
Ilimi naji daɗin baituka.

8. Ka amince min nayi gargaɗi,
Da yabo, da nasihata duka,

9. Kuma kana na jero ni’ima
Falalar Kur’ani, dan haka,

10. Ku biyoni kusha baiti na Ka
Farkonshi da “K”, karshenshi “ka”:

11. Kur’ani kundin mumini

Tushen asalin maluntaka!

12. Ku rikeshi makami kar ku ki,
Ku zubarda takobi har baka.

13. Ku sakashi yazamto magani
Cuta a jikine, ko a ka.

14. Ku rikeshi maceci ko'ina
Ceto ga waliy kar kuy haka!

15. Ku sanifa Waliyyi Mumini.
Mai tsoron Allah ne duka.

16. Ku tuno maganar Allah a can
Da yace ceto ba mai maka.

17. Koda manzo ne ko Waliy!
Sai Allah ya yarje maka.

18. Ku sani Kur'ani yai gaba
Yafi karfin mai bokantaka,

19. Kundin wahayi daga Rabbana
Kur'anin Manzo mai Maka.

20. Kaidai malam ɗan dakata!
Wannan zikiri ya ɗaukaka,

21. Ka sani harafi ɗaya goma ne
Ladanshi, idan ka san haka.

22. Kam karfin jarin ya isa
Kuma ribar har ta tsallaka.

23. Kuma Manzon tsira ya faɗa
Makaranta Kur’ani duka,

24. Kenan matansu da ma maza
Ka haɗa manya da kananuka,

25. Kimar ladansu ga Rabbana
Matsayi-matsayi ne su duka,

26. Ku sani amma shikam Gwani
Matsayinshi kwarai ya ɗaukaka,

27. Kuga tsara nashi Mala’iku
Manya sosai kumu san haka.

28. Kuma shi kuma mai koyo da kyar
Ladanshi kala biyu sau haka!

29. Kumu ɗauki misali kunjiya,
Na gidaje koko gini duka,

30. Kuga shi rayayyene gini;
Indai Kur’ani an saka.

31. Kuma tamkar gawane gida;
Mara sautin Kur’ani duka.

32. Kai ga wata sura Bakkara
Falalarta da dama, dan haka,

33. Ka karanta kai da ɗiya naka
A gida ne koko cikin ɗaka,

34. Ka tsira da sharrin makiri
Shaiɗani baya shiga maka.

35. Kaf in muka duba zamuga
Masanan Kur'ani su duka,

36. Koda tsoho ko jinjiri,
Ya zam gwarzon jarumtaka.

37. Ku biyoni kuce Alarammiya-
Alaramma mutum mai ɗukaka.

38. Kai bar shima ɗauko uban
Ka haɗo innarshi kamar haka,

39. Kimar matsayinsu ga Rabbana
Kama daga ɗan ka haɗa duka,

40. Kambu ne za'a naɗa masu
Rawanin haske mai haskaka,

41. Kuma Al'arshe inuwa guda
Sun zauna su da jinin Maka.

42. Kuga ai girman ya girmama
Kaskanci ba kaskantaka.

43. Ka sani Kur'ani shi kaɗai
Hujjane kanka, kasan haka.

44. Kuma hujja gunka idan kayo
Koyi na faɗarsa da ayyuka.

45. Kowa ya sakeshi: yasha wuya,

Kowa ya rikeshi: ya ɗaukaka.

46. Ku sani falalar Kur'anuna
Da yawa ne, sunfi gaban haka.

47. Kak kwana a nawa. Saboda ni
Adami ne! Gara kasan haka.

48. Kaf-kaf falalar da na ɗan faɗa
Basu kai ashirin ba cicif duka.

49. Kama ka rike ka dada a kan
Kimar kimanin baituka.

50. Kuma sai ka yi dimbin addu'a
Ga Abu Yasir na Amerika.

51. Kakan yaran islamiyya
Onlayin komai ya saka.

52. Kan TouTube je ka ka bincika
Ka bi dukka sauran shafuka.

53. Kuma dan haka nan gun zan tsaya
Domin nasan na tabuka!

54. Kammalat wa tammat dan haka
Ni na tafi, sai baɗi war haka.